Cewa wani mutum ya yi alwala, sai ya bar tabo (Lam’a) gurin farce a kan ƙafafunsa, sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya gan shi (wurin) sai ya ce: "Koma ka kyautata alwalarka" Sai ya dawo, sannan ya yi sallah

Daga Jabir - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Umar Dan Alkhaddab ya bani labari: Cewa wani mutum ya yi alwala, sai ya bar tabo (Lam’a) gurin farce a kan ƙafafunsa, sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya gan shi (wurin) sai ya ce: "Koma ka kyautata alwalarka" Sai ya dawo, sannan ya yi sallah.
[Ingantacce ne a baki dayan ruwayoyin sa] [Muslim ne ya rawaito shi]

Umar - Allah Ya yarda da shi - ya bada labarin cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ga wani mutum ya gama alwalarsa, sai ya bar gwargwadan farce a ƙafarsa (Lam’a) ruwa bai same shi ba, sai ya ce masa yana mai nuni zuwa gurin da bai sami ruwa ba: Ka koma ka kyautata alwalarka ka cikata ka ba wa kowacce gaba haƙƙinta na ruwa. Sai mutumin ya koma ya cika alwalarsa, sannan ya yi sallah.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/8386